

# Alheri Na Bukatar Wani




Aisha Ahmed Jada
Mai Rubutu

Benjamin Garba
Mai Fassara

# Alheri Na Bukatar Wani



Aisha Ahmed Jada
Mai Rubutu

Benjamin Garba
Mai Fassara

Dauda Bello da Karon Harden, Editoci


STELLAR
American University of Nigeria

Published by:
STELLAR (STudents Empowered through Language, Literacy, and ARithmetic)
American University of Nigeria
Lamido Zubairu Way, Yola By-Pass
Yola, Adamawa State, Nigeria PMB 2250
http://www.americanuniversitynigeria.org

This book is a translation from English to Hausa of *One Good Turn Deserves Another* by Aisha Ahmed Jada © 2014 American University of Nigeria / CC-BY-3.0 (see creativecommons.org/licenses/by/3.0/).

**Alheri Na Bukatar Wani (Hausa)**
© 2014 American University of Nigeria / CC-BY-3.0
Permission is granted to download, copy, adapt, translate, and/or distribute this book in any media, with attribution to the original author(s), translator(s), illustrator(s), publisher, and funder(s), where applicable, under the terms of the Creative Commons Attribution 3.0 Unported License. For separate use and/or adaptations of the images contained within this book, please refer to their individual permissions as specified under Image Credits.
Electronic copies of this and other books are available for free at:
www.americanuniversitynigeria.org/about/dev/stellar

Image Credits:
All images from © 2009 SIL International / International Illustrations: The Art of Reading 3.0 / CC-BY-ND-3.0 (see http://creativecommons.org/licenses/by-nd/3.0/




Ga tanan ga tananku. Ku zo mu ji ta.

An yi wata ‘yar maraya, mai sunan Saratu wadda take zama da kishiyar mamarta tare da ‘yar kishiyar matarta ɗin, mai suna Bolu, a wani ƙaramin ƙauye.

Saratu tana da ladabi da biyayya kuma ba ta ƙiwuya, amma Bolu tana da banzan hali da rashin kunya, ga ta kuma da yawan ƙiwuya.

Kishiyar mamar Saratu ɗin nan kuma, tana yi da Saratu kamar yadda ta ga dama cikin wulaƙanci har wasu lokatai Saratu ta sa ran za ta gudu ta bar gida, amma ba ta da wurin zuwa.







Saratu tana yin dukan ayyukan cikin gida, amma kishiyar mamarta ba ta nuna godiya.

Sai dai daɗa musguna mata take ta yi a kan kome.

A kan hakan ya sa Saratu kullum zaman cikin baƙin ciki take yi.







Wata rana da tsakar dare, kishiyar mamar Saratu ta aiki Saratu ta je ɗiban ruwa a kogi.

Cike da tsoro, Saratu ta je ta ɗebo ruwan tun da ya zama mata tilas.




A kan hanyar dawowa, ta gamu da wani tsoho wanda ya bukaci Saratu ta ba shi ruwa ya sha.


Saratu kuma ta ba shi ruwan daga ƙwaryarta.


Sai kuma ta tambaye shi da cewa, “Mallam, na ga kana nan da dare kai kadai.  Kana bukatan taimako ne?”



Amma tsohon ya amsa mata, ya ce, “ A’a, ‘yata, amma domin alfarmar da kika yi, ki kalli nan.” Tsohon ya nuna mata kwalaye uku masu faɗi daban-daban. “Ki zaɓi ɗaya daga cikinsu, ya zama kyauta zuwa gare ki, amma kada ki buɗe sai kin isa gida.” Sai Saratu ta zaɓi kwali mafi ƙanƙanta a tsakaninsu, sai ta kama hanya, ta tafi gida.











Da ta isa gida, sai ta shiga ɗakinta, sai ta buɗe kyautar da tsohon ya ba ta.  A cikin kwalin nan kuma ta sami kuɗi da gwala-gwalai da riguna da waɗansu kyawawan abubuwa.

Saratu ta yi farin ciki matuƙa, sai ta kira kishiyar mamarta da 'yarta Bolu su zo su gani.





Sun yi mamaki ƙwarai da gaske. Sai suka tambaye ta a ina ta samo waɗannan.

Sai Saratu ta gaya musu labarin tsohon da suka sadu a hanya, ya yin da take dawowa daga ɗiban ruwa a kogi.



Sai kishiyar mamar Saratu ta gaya wa ’yarta Bolu, “Ki je ke ma ki ɗebo ruwa a kogi, za ki dawo da waɗannan kyawawan abubuwan irin na Saratu, har ma fiye da haka.” Bolu ta yarda, amma dai domin yawan kwaɗayi da son kanta.  A kan hanya tana ta guna-guni da kuma zagin Saratu domin ita ta jawo mata zuwa kogi da dare ɗiban ruwa.




Sai ta zo ta gamu da tsohon yana zaune a ƙasa. Sai ta miƙe a guje zuwa wurinsa. Sai ta ambace shi ya ba ta nata rabon abubuwan da ya ba Saratu.  Sai tsohon ya ce mata, "'Yata, don Allah, ki taimake ni ki ɗaga ni na tsaya."


Sai Bolu ta ƙi, ta ce, "Wane irin wawan rago ne wanda zai zo kogi da dare shi kaɗai bayan da bai iya tashi a tsaye da kansa ba?"




Sai tsohon ya nuna mata kwalaye guda uku masu faɗi daban-daban sai ya ce, “Ki zaɓi duk wanda kike so a tsakanin kwalayen, sai ki tafi gida.”

Domin yawan kwaɗayi da son kanta, sai ta zaɓi babba daga cikin kwalayen, sai ta juya a guje da gudu ta koma gida ba tare da godewa tsohon ba.












Da Bolu ta isa gida, sai mamarta ta yi farin ciki da ganin ‘yarta da kwalaye a hannunta. Sai ta ce ma ‘yarta su yi maza-maza su shiga ɗakinta domin su buɗe su ga abubuwan da ke ciki tare.

Amma suka yi mamaki da suka buɗe, sai suka ga macizai, gizo, kunamu, da waɗansu dabbobi masu ban tsoro. A taƙaice, sai dabbobin suka ciccije su, suka kuma harbe su, sai suka yi rashin lafiya na mako ɗaya.

Daga wannan ranar, Bolu da mamarta suka fara jin tsoron Saratu, suna kuma girmama ta.

Sai suka daina sa ta aikin gidan ita kadai, sai dai su haɗu su yi shi tare dukkansu, kaman iyali.

Sai Saratu ta yafe su da munanan halayensu, ta kuma raba kayanta tare da su.







**Tambayoyi**

1. Yaya rayuwar Saratu take tare da kishiyar mamarta da ‘yar kishiyar mamarta?
2. Yaya Saratu ta bi da tsohon nan da suka haɗu a hanya lokacin da take dawowa daga kogi?
3. Wane irin kwali ne Saratu ta ɗauka? Mene ne a cikin kwalin?
4. Yaya Bolu ta bi da tsohon nan?
5. Wane irin kwali ne Bolu ta ɗauka? Mene ne a cikin kwali?
6. Don me kuke tsammanin kwalin Saratu da na Bolu sun bambamta?
7. Me ya faru a ƙarshen labarin?

Bayani Ga Iyaye:
Sau da yawa bincike ya nuna cewa koyon karatu a harshen da yara suka saba, watau harshensu, na garinsu, ko na al'ummarsu, yana taimako sosai wajen ƙara masu saurin koyo da kaifin fahimta. Mafi yawan yara da suka fara karatu da harshensu suna fin sa'o'insu da ba su fara da harshensu ba a karatun wani harshe. Misali, idan yara masu jin hausa sun fara karatu da hausa, karatun hausa zai taimaka sosai wajen koyon karatun turanci. Haka kuma yara za su fi fahimtar kalmomi da ma'anarsu na sabon harshe idan sun sami matashiya a nasu harshen. Matakin da ya fi dacewa ku ɗauka na inganta karatun yaranku shi ne ku kwaɗaita masu karatu kullum a harshensu kafin su fara koyon turanci, kuma su ci gaba da karatu.